M
I
A
U

(١)

## AIKI DA HANKALI WAJEN FAHIMTAR NASSI:

## (IMAM ABU HANIFA DA MAKARANTARSA)

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Littafi ne mai albarka da muka saukar maka; saboda su yi tunani na tadabburi game da ayoyin cikinsa, masu hankali kuma su wa'aztu)** [Sad: 29]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai addinin Musulunci ya muhimmanta hankali yanda ya kamata, saboda hankali ne majingina takalifi, haka ma kiyaye hankali yana cikin manyan manufofin Shari'ar Musulunci, ɗaya daga cikin manyan ƙa'idoji, kuma ginshiƙai guda shida da dukan shari'o'i, da addinai suka haɗu akan a ba su kariya.

Lallai Ubangijinmu ya shiryatar da mu zuwa ga yin amfani da ni'imar hankali wajen yin tunani, da lura game da zahirin halittun Allah, domin mu samu mu gano girmansa mai girma da ɗaukaka, da kuma kaɗaituwarsa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai a cikin halittar da Allah ya yi wa sammai da ƙasa, da abubuwan da suke cikin su na ƙwarewa da gwaninta, da saɓanin da dare da rana suke da shi, na haske da duhu, tsawo da gajerta, akwai bayyanannun ayoyin ga masu hakalin da suke iya riskar kaɗaitakar Allah da ikonsa)** [Ali Imran: 190], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(A cikin ayoyinsa akwai**

**halittar sammai da ƙasa, da kuma bambancin harsuna da launin fata da kuke da su, lallai akwai manyan ayoyi game da haka ga masu ilimi masana)** [ar- Rum: 22], duk mai bibiyan bayanan da Alƙur'ani ya zo da su zai iya riskar irin yanda Allah mai girma da buwaya yake kwaɗaitar da hankalin ɗan Adam zuwa ga yin tunani, da salo iri- iri, irinsu inda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **(Ko zai sanya ku yi tunani), (shin mai zai hana ku yi tunani ne?), (Ga mutanen da suke tunani), (ga mutanen da suke da hangen nesa), (ga mutanen da suke fahimta).**

Duk wanda yake yi wa Shari'ar Musulunci kallo na lura zai iya ganin irin yanda ta kwaɗaitar zuwa ga yin aiki da hankali ta hanyar yin ijtihadi, da fitar da hukunce- hukuncen Shari'a daga cikin dalilai da suka zo dalla- dalla, abin da zai kai zuwa ga sauƙaƙa wa mutane rayuwa, ya kuma gyara al'amurransu na duniya da na lahira, tare kuma da kiyaye tabbatattun abubuwa na Shari'a mai daraja, ko ginshiƙai da ba sa sauyawa, waɗanda ba a taɓa su, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Idan shugaba ya yi hukunci na ijtihadi, sai ya yi daidai, to yana da lada biyu, idan kuma ya yi hukunci na ijtihadi ya yi kuskure, to yana da lada ɗaya)**.

Babu shakka kan cewa Imam Abuhanifa an- Nu'uman (Allah ya ƙara masa rahama), mai shahararriyar mazhabar nan ta Hanafiyya, jagora ne na makarantar da take aiki da hankali wajen fahimtar Nassoshin addini, Allah Maɗaukakin Sarki ya azurta shi da cikakken hankali mai kiyayewa, ba ɗan bita- zaizai ba ne shi, bai kuma tsayawa akan doron Nassi; hasali ma duba yake yi zuwa ga manufofi, da abubuwan da Nassi yake nufin tabbatarwa, saboda haka ne ya zama shugaba, kuma jagora a makarantar aiki da hankali wajen fahimta, da ta'amuli da Nassoshi (Allah ya ƙara

yi masa rahama), abin da har ya kai ga malamai suna faɗin cewa: Gaba ɗayan mutane sun yi kalacensu ne a Fiƙihun Abuhanifa.

Lallai Imam Abuhanifa (Allah ya ƙara yi masa rahama) a Fiƙihunsa ya kula -ƙwarai da gaske- da zamani, gami da wuri, da kuma yanayin da mutane suke ciki, da al'adunsu, da ɗabi'unsu, sai ya zama cikin waɗanda suka yawaita yin aiki da "al-Ƙiyas", da "al- Istihsan", da kuma "al- Urfu", yana mai kafa hujja da Hadisin Sayyiduna Mu'az (Allah ya ƙara yarda da shi), lokacin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya tura shi Yamma, ya ce masa: **(Da mene za ka yi hukunci?)**, sai ya ce: Da littafin Allah Maɗaukakin Sarki, sai ya ce: **(Idan ba ka sami hukunci a cikin littafin Allah ba fa?)**, sai ya ce: Da Sunnar Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), sai ya ce: **(Idan ba ka sami hukuncin a cikin Sunnar Manzon Allah ba fa?)** sai ya ce: Zan yi ijtihadi da ra'ayi na, sai (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Lallai na gode wa Allah da ya datar da ɗan saƙon Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam)**, da dai sauran Hadisan da suke kwaɗaitar da yin aiki da hankali wajen fahimtar Nassoshi, ƙarƙashin manyan manufofin Shari'a da suka game komai da komai.

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai addinai sun zo ne domin su sanya mutane cikin jin daɗi, ba domin su wahalar da su ba, Allah Maɗaukakin Sarki yana

cewa: **(Ya Ɗaha, ya Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), ba mu saukar maka da Alƙur'ani domin ka wahala ba)** [Ɗaha: 1- 2], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Allah bai sanya maku wata wahala a cikin addinin Musulunci ba)** [al- Hajji: 78], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai Allah sauƙi yake so maku, ba ya sonku da wahala)** [al- Baƙra: 185], ba a taɓa bai wa Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) zaɓi tsakanin abubuwa guda biyu ba, face ya zaɓi wanda ya fi sauƙi, matuƙar dai ba saɓo ba ne, idan saɓo ne shi ne ya fi kowa nesantarsa; saboda haka, babu wani abu da zai sanya a wadata da aiki da hankali wajen fahimtar Nassoshi, da wurin aiki da su, da wurin saukar da hukuncin Allah a wurin da ya dace a aikace.

Lallai muna ƙara tabbatar da cewa ya kamata malami ya zama ya san al'amurran zamaninsa, da sababbin abubuwan da suke faruwa, ya kuma san yanayi, da halayen mutane, da al'adunsu, saboda ya sami daman bayar da fatawar da ta dace da yanayi, gami da halin da zamanin da aka yi ta yake ciki, ba wai ta yi daidai da wasu zamunna, ko wurare na daban ba, duk wanda ya bai wa mutane fatawa ba tare da ya yi la'akari da yanda zamaninsu, da garinsu, da ɗabi'ar rayuwarsu suke ciki ba, to kuwa babu shakka ya bijirar da rayuwarsu zuwa ga wahala, gami da takura, a daidai lokacin da Shari'armu mai cike da haske kuma ta ginu ne akan sauƙi, da yalwa, da kuma ɗauke damuwa.

**Ya Allah Ubangiji ka ƙara fahimtar da mu al'amurran addininmu, ka kuma kiyaye mana ƙasarmu da sauran ƙasashen duniya.**